Jan hannun ta tayi suka nufi kitchen suka fara preparing girke girken Abinci kala Uku, Cikin *2hours* da y'an mintoci suka kammala komai, sannan suka jera a dinning table cike da Fara'a. Yaya Farook fitowa yayi daga d'aki cikin hanzari ya wuce masallaci , Acen yayi Magrib sannan Ya dawo. Fadwa tsayawa tayi a bakin

kofa Tana jirar isowar Abba ' bud'e k'ofa taji anyi hakan yasa tayi saurin jan handle din gami da cewa,

"Oyoyo Abb....

kasa k'arasa maganar tayi ganin Cewar ba Abba bane ya dawo Yaya Farook ne ya shigo, Cikin tsoro da sanyin jiki tace.

"I thought Abba ne ya dawo shiyasa....

Harara ya balla mata tare da jan tsaki ' sannan ya je wajen dinning table yayi zaman shi, Itama komawa tayi ta zauna Ilham kuwa babu abinda takeyi inbanda dariya.

*_Kuyi_* *_hakuri_* *_wannan_* *_Don_* *_bashida_* *_Yawa_*

Dedicated *To* *My* *Fan's*

□□□😉

[4/18, 3:55 PM] Maman Ussey😘: .....□□□□□□□

□□ *BABBAN...GIDA*□□

□□□□□□□

*_P.W.F_*

© ```Written```

By

*_Seemaluvv_*□

15-16 pages□

Suna cikin Haka ne Umma ta shigo Parlon Ta sami Waje ta zauna Sannan Ta kalli Fadwa ' Ganin yadda jikin ta duk yayi sanyi,

"Fadwa ya naga duk jikin ki yayi sanyi? Ko Halan Farook ya dake ki?

Cewar Umma,

Saida Ta kalli Yaya Farook sannan Ta girgizawa Umma kai alaman A'a, Suna cikin Wannan ne Sukaji Sallama Abba ' Ilham ce tayi zambur ta mik'e tsaye tare dayin Ihu,

"ahhh!!! Yeee Abban mu ya dawo.

Gaba d'ayan su Mik'ewa sukayi tsaye cikin murna suka tunkare shi, Ilham ta karb'a jakar hannun shi tare da cewa.

"Abba sannu da dawo wa!

Amsawa yayi Cike da fara'a sannan ya kalli Fadwa wacce ta rakub'e a bayan Umma ita a dole ta na fushi,

"Haba Wa ya tab'amin Y'ata Fadwa?

Cewar Abba,

Nan ta saki Fuskarta Tayi murmushi sannan ta ce,

"Abba kaine Kaimin Laifi da baka dawo da Wuri ba ' amma Yanxu Tunda Kadawo shikenan.

Gaba d'ayansu dariya sukayi sannan suka nufi Dinning Table domin cin abin, Ilham kuma sashen Umma ta nufa Domin ta ajiye jakar Abba.

Bayan Sun zauna ne ' Fadwa ta fara Yimasu Sarving Abincin, Sai da tabbatar ta zubawa kowa sannan Ta koma tazauna itama Ilham ta zo ta zauna suka fara cin Abinci ' Abba kallon Yaya Farook yayi sannan ya kuma kalli Ilham da Fadwa,

"Fadwa??

Abba ya kira sunan ta cikin kamala ta d'ago kai ta kalle shi tare da cewa,

"Na'am Abba.

"Naga kin rame mun ne, A kwai mai takura maki ne?

Abba na fad'in haka ta kalli Yaya Farook taga shima ita yake kallo ko zata ce wani abu,

"A'a Abba babu mai takura mun, nayi rashin Lafiya ne.

Ta na gama rufe baki Umma tayi sauri ta ce,

"Karki wani boye mashi ' babu mai takura maku inbanda Farook.

"Haba Umma ki barta ta fad'a Da bakinta mana , ai ita tasan babu abinda nake mata.

cewar Yaya Farook,

Shuru kawai Fadwa tayi ta sunkuyar da kanta.

"Hmm aini dama Nasan za'a rina Wannan zaman gidan naka wasane? Ainasan duk wannan bak'in halin kansu zai kare.

Abba na gama fad'an haka Fadwa ta mik'e tsaye da niyyar wuce wa d'akin su.

"Ina kuma zakije?

Cewar Ilham,

"Wallahi bacci nakeji sosai ' shiyasa zanje in kwanta.

"Tohm nidai bacci ba yanzu ba,

Fadwa d'aukan plate d'inta tayi tare da yiwa Umma da Abba sallama , sannan ta kad'a kanta ta wuce d'aki.

Bayan Wuce warta ne da y'an mintoci, Yaya Farook shima ya tashi gami da yimasu sallama ' kai tsaye ya wuce d'akinsu Ilham, Ko sallama bai yiba yana shiga ya iske Fadwa har tayi shirin bacci rigar bacci ne ma a jikin ta ' tana zaune a kujerar Madubi.

Ganin mutum kawai tayi a tsaye a bayanta, hakan yayi matuk'ar bata tsoro ' a firgice ta mik'e tsaye tana shirin yin ihu yayi saurin Toshe mata baki,

"Are you out of your sense? Akwai wanda zai shigo d'akin nan bayan nine?

Girgiza mashi kai tayi sannan ya sake mata baki ',

"Yaya Farook Lafiya?

Tayi tambayar ta na kallon idon shi,

"Fadwa meyasa bakiyi sallama dani ba kafin Kije ki kwanta?

Yayi maganar a sanyaye ' ita kanta saida tayi mamaki,

"Am sorry Yaya Farook.

"Ba kya tunanin halin da zan shiga?

Zaro idanu tayi cike da Mamaki a zuciyar ta tace,

"Oh ni Allah Yau kuma Yaya Farook ni yake fad'awa haka.

K'ara matsowa yayi dafff da ita suna shak'an numfashin junan su, sannan ya riko habar ta.

"Am totally in love with you Fadwa ' am in love with your dress,

Abun ne ya bata tsoro ganin yadda ya sauya lokaci d'aya gashi kuma su biyu a d'akin hakan yasa ta cewa,

"Yaya Farook please Kaje kada Ilham ta zo ta sameka a nan wajen kaji.

Saurin sakin ta yayi tare da cewa,

"Tor Promise me that we will Always be together.

Kai ta d'aga mashi Tare da cewa,

"I promise you that i will always be with you!!

Tana gama fad'in haka Ya juya Ya fita daga d'akin ya wuce d'akin shi.

Bayan fitan shine Ilham ta shigo d'akin a tsaye ta sami Fadwa,

"Kinyi wani tsaye kamar soldier ' ya akayi.

ta fad'a tana kokarin cire rigar jikinta don sanya ta bacci, Murmushi kawai Fadwa tayi sannan ta ce.

"I think am in love with him.

ta fad'a tana k'ok'arin Hayewa saman gado, Cikin sauri Ilham ta sanya rigar bacci itama ta d'are saman gadon Tare da zurawa Fadwa ido,

"In love with who ' Fadwa?

"No lokaci baiyi ba tukunna Ilham ' kibari sai lokaci yayi sai in fad'a maki.

Ya tsine Fuska tayi gami da jan pillow,

"Kyadaiji dashi kuma idan tayi wari aizanji.

Cewar Ilham,

smilling Fadwa tayi sannan suka kwanta.

*** *** *** *** ***

Washe *Gari* ...

Da sassafe Fadwa ta farka daga bacci ' Jitayi tamkar an d'ora mata dutse a marar ta saboda Azabar Ciwo,

"Ahhhghh Ilham don Allah ki tashi ki taimaka min,

Cikin Magagin bacci Ilham ta farka , Ganin yadda Fadwa keta hawaye ne yasa Baccin idon ya washe.

"Meke damunki?

"Menstrual cramp, ke damuna Ilham please... ki bani pain reliever please.

Cikin hanzari Ilham ta diro daga gado taja side drower ' ta ciro Paracetamol ta bata, sannan ta nufi Kitchen ta d'auko ruwa ta kawo mata. Bayan ta sha maganin ne ta tashi cikin dabara Ta sanya Pad (Always) a jikin ta sannan ta koma ta kwanta , bacci yayi awon gaba Da ita.

Ilham Bathroom ta shiga tayo wanka tukunna ta fito ta shirya ' Sannan ta wuce Kitchen don ta had'a Breakfast, Cikin Sauri ta had'a tea tazuba cikin Plask takawo parlor ta ajiye, Su Umma da Abba suka shigo cikin Parlon Suka zauna sannan Ilham ta gaishe su.

"Ina Fadwa??

Cewar Umma,

"Umma Tana daki batajin dad'i Menstrual cramp ke damunta.

"Subhanallah to tasha magani daiko?

Cewar Abba,

Kai Ilham ta d'aga mashi Alaman Eh sannan ta zuba masu Tea din Ta basu, Itama ta cigaba da shan nata tea din. Bayan ta gama breakfast d'inta ne ta wuce d'aki domin tayi shirin wucewa School, Tana shiga ta d'auki Handbag d'inta sannan ta juya ta fito daga d'akin.

Ta na fitowa suka had'e da Yaya Farook, ta gaishe shi sannan ta juya Zata wuce Yayi saurin dakatar da Ita da cewa.

"Ita Fadwa bazata je School d'in bane yau?

"Eh Batada Lafiya ne!

Ok Kawai ya ce mata sannan tayi tafiyar ta.

Dedicated *To* *My* *Fan's*

□□□😜

[4/18, 3:55 PM] Maman Ussey😘: .....□□□□□□□

□□ *BABBAN...GIDA*□□

□□□□□□□

*_P.W.F_*

© ```Written```

By

*_Seemaluvv_*□

@*JAMEESHA* *_wannan_* *_page_* *_d'in_* *_nakine_* *_i_* *_just_* *_feel_* *_like_* *_dedicating_* *_this_* *_page_* *_to_* *_you_* *_because_* *_of_* *_love_* *_and_* *_friendship_*

19-20 pages□

Bayan wasu y'an lokuta k'alilan ne Umma ta ga kiran Yaya Khaleel ya shigo cikin Wayarta, Murmushi tayi gami da girgiza kai tukunna ta d'auka,

"Sallamu Alaykum, "

"Hello Umma!? Umma yau zan dawo gida in sha Allah."

"Tor Khaleel Allah ubangiji ya tsare ' har jirgin naku ya tashi ne?"

"A'a Umma But yanzun nan zai tashi ' shiyasa nakira!"

Addua Umma tayi mashi sannan sukayi Sallama ta kashe wayar. Umma tashi tayi ta wuce d'akin su Ilham ' koda ta shiga Fadwa ce kawai tagani,

"Fadwa Ina Ilham? "

Cewar Umma,

"Umma Ta shiga wanka ne,"

"To idan ta fito Kice mata ' kushiga kitchen ku shiryawa Khaleel Abinci, don yau zai dawo."

😱To kawai Fadwa tace sannan Umma ta juya ta koma parlor ' nan wajen ta tsaya tana kokwanto akan Maganar Umma,

"Kai Kardai Yaya Khaleel dinda Ilham ta bani labari? Wayyo ' shikenan mumbanu "

Cikin hanzari ta mike tsaye ' Ba tare da tasan abinda zatayi ba , kai da komowa kawai takeyi ' tana cikin hakan ne Ilham ta fito daga bathroom dauke da karamin towel a hannun ta tana goge gashin kanta, ganin yadda Fadwa keta yawo a dakin ne yasa ta tsaya cak ta na kallon ta.

"I hope ba wani laifin kika kara Daukowa kanki ba?"

Cewar Ilham,

Tsayawa tayi ta kalleta with sad face ' sannan tace,

"Kin fito kina wani Goge gashi ' verysoon zaki manta da wannan ai!!"

"Me kike nufi?"

"Eh Umma tace Mu shiga kitchen Mu shiryawa Yaya Khaleel abinci ' don ya kusa dawo wa,

"What!!?"

Cikin tsawa da muryar tsoro tayi magana ' Hakan yasa ta samu waje ta zauna a sanyaye tare da cewa,

"Shikenan, ya dawo Lafiya ' basai na shiga harkar shiba sannan zansha wuya?"

Shuru sukayi nadan lokaci sannan Ilham ta ce,

"Please Fadwa kije kifara Kafin Ingama shiryawa ' koma mene ne sai indaura daga baya."

Ok kawai Ta ce mata sannan ta fita daga Dakin Zuwa kitchen.

Around *3:00pm*

Bayan Fadwa da Ilham sun kammala Komai sun jera a dinning table ne ' Abba ya dawo Gida,

"Anata preparation din dawo war Khaleel ne?"

Yayi magana cikin sauri ya na k'ok'arin wuce wa sashen shi, Ilham ta d'ago kai ta kalle shi cikin sanyin jiki.

"Eh Abba wai haka aka ce."

Komawa sukayi suka zauna a harabar Parlor suna kallon, Yaya Farook ya shigo d'auke da leda Guda biyu a hannun shi ' Wurgama ko wannen su yayi Fuska a daure ya sami waje ya zauna.

Cikin sauri Fadwa ta bude ledarta da kwalin waya ta fara hada ido ' xambur ta mike tsaye cike da murna,

"Wayyoo Yaya Farook..."

Juyowa tayi ta kalleshi cike da Fara'a, ganin ya daure fuska ne yasa Ta koma a zaune jiki a sanyaye. Itama Ilham bude nata tayi taga wayace ' sannan tayi mashi godiya, kai kawai ya daga Mata alaman Yaji ' sannan yace,

"Yau Khaleel zai dawo Hope ' kun kammala komai."

A tare suka amsa da cewa Eh, Sannan kowannen su ya mik'e tsaye d'auke da wayarshi a hannu suka wuce d'aki. Shima Yaya Farook tashi yayi ya wuce d'akin shi, yana shiga ya ciro wayar shi ' yayi dailing wata new Number.

Fadwa na zaune bayan sun kunna wayan ' cikin jin dadi Itada Ilham sai taga kira ya shigo Wayar,

"Kai!! Ilham harda Sim a ciki."

Abunda ta ce kenan ' tayi saurin yin recieving call din, Sai jitayi ance.

"It's Me Farook, kizo d'akina Yanzun nan."

Yana gama fad'in haka ya kashe wayar, kallon Ilham tayi Cike da mamaki.

"Wane ne?"

Cewar Ilham,

Smilling tayi mata ba tare da tace mata komai ba ' ta tashi ta bar d'akin, kai tsaye ta wuce dak'in Yaya Farook ' saida tayi knocking sannan ta shiga tare dayin Sallama,

"Yaya Farook gani!

Juyowa yayi ya kalleta ' sannan ya jawo hannun ta ya zaunar da ita a saman gadon shi,

"I hope kinji dad'in Gift d'inda na baki?"

Ya fad'a yana k'ok'arin zaunawa kusa daita,

"Eh Yaya Farook na gani ' kuma na gode sosai"

"Fadwa you completely changed my life ' koda nayi niyyar yin wani abun saboda Soyayyar ki sai inji nakasa, because i love you so much."

Yana gama fad'in haka yayi kissing d'inta a goshi,

"Tashi ki wuce d'aki, bazan iya jore ganin ki a nan wajen ba ' komai zai iya Faruwa Fadwa!!"

Cikin Sanyin Murya yayi Maganar ' hakan yasa taji wani Yarrrrr a jikinta, da sauri ta mik'e sannan ta bar d'akin cikin hanzari. parlor ta wuce kai tsaye ' Suka had'e da Umma zataje kitchen,

"Lafiya Fadwa? Naganki kamar Wacce aka biyo ne?"

Had'd'iye miyau tayi daker, tare da zurowa Umma idanu tana tunanin k'aryar da zatayi mata.

"Fad'amin mana, Don Fuskarki ta kasa boye tsoron da take d'auke dashi, "

"Amm...well Umma babu komai ' and please don't worry about me, tsaka nagani a kitchen shiyasa naji tsoro."

"To shikenan Allah ya kyauta."

Ameen Ta ce sannan ta k'arasa Parlor ta zauna ' zamanta keda wuya taji ana Knocking K'ofa, tashi tayi taje ta bud'e. Cikin izza ya shigo Cikin parlon ' Fadwa baki ta saki ganin yadda ya shigo kai tsaye,

"Malam lafiya? Kuma wa kake nema? "

Juyowa yayi ya kallet ta cikin b'acin rai da jin haushin tambayar da tayi mashi, yasa ya dawo daff da ita ya tsaya tare da k'are mata kallo.

"Ke? .."

Kasa k'arasawa yayi saboda haushi, sannan ya juya zai k'arasa cikin gidan tayi sauri ta rike mashi riga.

"Malam magana nakeyi ai...."

Ji kake Tasss ' tun kafin ta gama rufe baki ya sharara mata mari,

"ke!! Wace ce dazaki yimun irin wad'an nan tambayoyin, Koda yake dama haka y'an aiki suke ' To nine Khaleel kuma idan kika cigaba da Yimun tambayoyi dukan banza zakisha."

Zukunna wa Fadwa tayi rik'e da fuskarta hawaye na gangaro mata ' Lallai ta tausayawa kanta jin Yadda sukayi Arba da Yaya Khaleel for the first time, Haka nan Ta share hawayen ta tare da mik'ewa tsaye.

"kayi hak'uri Bansan kaine Yaya Khaleel ba...

Tsaki ya ja gami da zama a saman kujera,

"Naji kije ki kiramun mutanen gidan."

Juyawa tayi ta nufi d'akin su ta iske Ilham a zaune, Ilham d'ago kai tayi ta kalle Ganin fuskarta babu annuri ne yasa tayi saurin mik'ewa tsaye,

"Fadwa? Ya dawo ko?"

"Hmm ya dawo mana ' tunda harya watsamin mari"

Zaro ido tayi sannan ta fita d'akin cikin sauri ta nufi kitchen ta fad'awa Umma, sannan ta zarce d'aikin Yaya Farook shima ta sanar dashi ' ita dai Fadwa zama tayi a bakin gado ' cike da jimamin marin da tasha.

Dedicated *To* *My* *Fan's*

□□□😉

[4/18, 3:55 PM] Maman Ussey😘: .....□□□□□□□

□□ *BABBAN...GIDA*□□

□□□□□□□

*_P.W.F_*

© ```Written```

By

*_Seemaluvv_*□

17-18 pages□

Bayan wucewar ta yayi sauri ya shiga cikin d'akin nasu, A kwance ya iske Fadwa rungume da pillow ta na bacci ' zuwa yayi ya zauna a gefen ta setin fuskar ta, a hankali yasa hannu ya shafa saman goshin ta tare da kissing d'inta a goshi.

Sannan ya tashi ya wuce parlor, a zaune ya sami Umma da Abba suna hira ' zuwa yayi ya tsugunna ya gaishe su sannan ya koma ya zauna.

"Ka karya kuwa Farook?

Cewar Umma,

"A'a Umma ban karya ba tukunna.

Yaya Farook maida kallon shi yayi akan Abba ' sannan ya ce,

"Ammm... Abba dama nazo ne natuna maka ' maganar Neman Aikin.

"Kaga Farook na manta aigwara daka tunamin ' kaje d'akina zakaga Wani envelop ka d'auko min.

Cikin hanzari ya tashi ya nufi d'akin Abba ' cikin minti Uku ya dawo d'auke da Envelop d'in rik'e a hannun shi, Sannan ya mik'awa Abba cike da ladabi.

"A'a rik'e a wajenka domin nakane, Wannan itace takardar samun Aikin naka Farook.

Murmushi yayi Har sai da hak'oran shi suka bayyana saboda jin dad'i ' cikin fara'a ya ce,

"Thank you so much Abba, nagode sosai Abba ' Allah ya bani ikon kyautata maku.

Ameen suka amsa a tare ' sannan Abba ya ce.

"A Company din Abokina ka sami aikin ' gobe Insha Allah zan kaika.

Cikin Farin ciki Ya tashi ya wuce d'akin shi ' nan ya dinga kiran Friends d'inshi suna Congratulating d'inshi. ya na gama wayar ya d'auki key d'in motar shi ya fita.

Around *10am*...

Fadwa ta farka daga bacci ' ta nufi bathroom tayi wanka sannan ta fito, Simple makeup tayi ta sanya doguwar rigar atamfa ' tukunna ta nufi parlor ta taradda Umma da Abba ta gaishe su sannan ta juya zata koma ciki Umma ta tsaida ita da cewa,

"Fadwa yaya jikin naki?

"Da sauk'i Umma.

"To Allah ya k'ara sauk'i,

Ameen ta ce sannan ta juya ta wuce.

kai tsaye ta nufi Lambu ta zauna tare d'aga kanta sama tana kallon yadda Tsuntsaye keta safa da marwa a wajen, abun Yayi matuk'ar burge ta yasa ta tashi ta k'arasa cen cikin Lambun tana kallon tsuntsaye kala dabam dabam.

Cikin ta ne ya fara mata k'ara sakamakon Karya wanda batayi ba, hakan yasa ta tsinki Tuffa(Apple) a wajen ta ci saida taji ta koshi sannan ta cigaba da kallon Cikin Lambun.

Yaya Farook dawo wa gida yayi ' Ya shigo parlor babu kowa sannan ya wuce cikin gidan, d'akin su Fadwa ya fara lek'awa ganin bata cikine yasa ya tafi Lambun shima kai tsaye, A zaune Ya hangi Fadwa ita kad'ai Fuskar ta cike da Fara'a, Ya k'arasa wajen ' jitayi anrufe mata Ido.

"Waye please? Ilham kece ko?

Shuru yayi ya kyaleta ba tare da yace mata komai,

"Mtsw Dalla malama ki sakemun ido na.

sake mata ido yayi sannan ta juyo ta kalle shi, ganin shine yasa ta tsorata ta mik'e tsaye gami sakin k'ara,

"Ahhghh, Yaya Farook kayi hakuri bansan kai bane.

D'aure fuska yayi ya matso daff da ita,

"Na sami Aiki Fadwa.

"Wow! Alhamdulillah Yaya Farook naji dad'i kuma na tayaka Murna.

Murmushi yayi Tare da tallabo fuskar ta da hannu biyu,

"Fadwa ai kece yadace azo a tayaki Murna ' Domin Wannan samun aikin tamkar ke ce kika sameshi.

Haka ya fad'a ya na k'ok'arin Kissing d'inta,

"Yaya Farook what are you trying to do?

Tayi tambayar gabanta na dukan uku uku, tana k'ok'arin Kub'uce wa ya k'ara matseta.

"Yaya Farook please ka daina mana ' banajin dad'in hakan....

Cikin sauri ya saketa Tare da juya mata baya yana maida numfashi, itama ta juya tayi gami da dafe k'irjin ta hannunta na rawa ta ce,

"Yaya Farook Am sorry but i just can't.

"Yes bazaki iya ba ai ' saboda bakya sona Fadwa.

Da sauri ta juyo ta kalle shi idanuwan ta sun kad'a sunyi jaaa.

"Yaya Farook na dad'e da fara Son ka a cikin Zuciya ta , kad.....

Bata kaiga k'arasa maganar ba Ya dakatar da ita da cewa,

"Inhar kina sona dagaske ' to kije ki fad'awa Su Umma domin suyi mana Aure, Fadwa baxan iya jure rashinki a kusa dani ba.

mamaki ne ya rufe ta ' yasa ta je Gaban shi ta tsaya,

"Yaya Farook kada ka d'auramun nauyin da banice Ya dace insauke shi ba.

Tana gama fad'in haka ta juya zata wuce yayi sauri ya rike hannun,

"Fadwa bazan iya fad'a ma Umma da Abba ina sonki ba.

Saurin fizge hannun ta tayi cikin bacin rai sannan ta juya ta wuce.

D'akin su ta wuce direct ' tana shiga ta fada saman gado, wasu zafafan hawaye ke zubo mata a fuskar ta,

"Wannan wace irin soyayya ce? Wannan wane irin azabtar wa ce? Dama haka Soyayyar take?....

Cikin kuka ta k'arashe maganar, tashi zaune tayi ta share hawayenta sannan ta wuce Kitchen ta daura girki.

*** *** *** *** ***

AROUND *1:56PM*

Fadwa ta gama girkin ta zuba cikin Plask ' sannan ta kawo parlor ta ajiye, ta wuce sashen Umma ta fad'a mata cewa ta gama Abinci, koda ta dawo iske Yaya Farook tayi a dinning table a zaune ' yana kallon ta cike da murmushi, Kawar da fuskar ta tayi sannan ta k'arasa wajen cikin sauri ta Zuba mashi abinci, fuskarta babu annuri a cikin ta. Bayan tayi sarving d'inshi ne ta koma ta zauna Suna kallon kallo,

"Bazaki zuba abincin bane?

Shuru tayi ta kyaleshi sannan ta zuba ruwa a cup tasha,

"Fadwa am i not talking to you?

"Am not hungry!

Abunda ta ce kenan ' ta mike tsaye da niyyar barin wajen yayi saurin tsaida ita,

"Fadwa son da nake miki bashine zai hanani hukunta ki ba idan kikayi laifi.

Cikin fad'a yayi maganar hakan yasa ta jin tsoro ' gudun kar jikinta ya dimamu ne yasa ta saki fuskarta tare da yin murmushi,

"Yaya Farook don Allah ka barni ' wallahi banajin Yunwa.

"Fadwa ban yarda ba ki dawo ki zauna,...

Yana gama fad'an haka Umma ta shigo parlon cikin hanzari Fadwa ta boye a bayan ta,

"O'o lafiya?

"Umma, Yaya Farook ne wai dole sainaci abinci yanzu ' ni kuma banajin yunwa,

"Ha'a Farook banason zalunci, antaba yin abune dole ne wai?

sosa kai yayi Cikin fara'a Sannan ya ce,

"Umma ni ban mata dole ba ni kawai...

Tun kafin ya k'arasa Umma ta ce,

"Yi tafiyar ki kinji ki kyaleshi,

Saida tayi mashi gwalo sannan ta juya ta wuce.

2:00pm

Bayan sun gama cin abinci ' Umma ta dawo harabar parlor ta zauna' shi kuma Yaya Farook ya d'auki key din motar shi ya fita, Ilham ce ta shigo cikin parlon a gajiye ' Ta gaida Umma sannan ta nufi d'akin su, ta na shiga ta Iske Fadwa a zaune ta na duba handOut. Zuwa tayi ta jiye Handbag dinta sannan tace,

"Ke baiwar Allah ya jikin naki?

Ajiye handout din tayi a gefe ta d'ago kai ta kalle ta,

"naji sauki kad'an Ilham.

"To gwara da kika warke da wuri don gobe munada test din Anatomy.

Cewar Ilham,

"Tabb hmm Allah dai kawai ya taimake mu kawai.

Ameen Ilham ta ce sannan ta dauki towel ta daura ' ta fada bathroom donyin wanka.

Dedicated *To* *My* *Fan's*

□□□😜

[4/18, 3:55 PM] Maman Ussey😘: .....□□□□□□□

□□ *BABBAN...GIDA*□□

□□□□□□□

*_PERFECT_* *_WRITERS_* *_FORUM_*

© ```Written```

By

*_Seemaluvv_*

23-24 pages

Washe *gari*....

Da sassafe around 6:22Am ' Fadwa da Ilham suka tashi sukayi Sallah, Bayan sun idar da sallah ne Ilham tayi wuff ta tashi tana k'ok'arin d'aura towel a jikin ta,

"Ilham kada kiyi wanka yanzu ' saboda gyaran d'aki yana jiran mu."

Cewar Fadwa,

Ilham tsayawa tayi tana kallon Fadwa d'auke da alaman tambaya a fuskar ta,

"Gyaran d'akin ina kuma? "

"Gyaran d'akin Yaya Khaleel kuwa, domin kuwa ya ce yau da safe zamu gyara shi ' Ai auna arzik'i mukayi jiya don wallahi da jikinmu ya gaya mana."

Tsaki Ilham taja ' tare da jan kwafa,

"To wallahi ' babu wani gyaran d'akin da zamu tsayayi, don kuwa test garemu yau ' shi ya gama nashi karatun mu zaizo ya takura mAna, "

"Tab!! To aini mantawa nayi banyi mashi bayani ba tun jiya d'in."

Ya tsine baki Ilham tayi gami da buga cinyar ta,

"ke kika sani, wallahi ki zauna nan harkisami Carryover ' shine na farko wanda zai jibge ki, "

Fadwa mik'ewa tayi tsaye tare da yaye hijab d'in jikin ta,

"To yanzu yaza'ayi kenan mu fita ba tare da kowa ya sani ba? "

"Yanzu dai kibari inshiga wanka ' infito saike ma ki shirya. "

Ilham harta juya zata shige bathroom Fadwa tayi saurin dakatar da ita da cewa,

"Ilham Amma kinsan dai bazamu fita ba tare da ' mun shirya musu breakfast ba ko?"

"Fadwa wai wane breakfast kuma? Bayan kinsan muddin muka tsaya tofa ' gyaran d'akin nan tamkar mun gama yin shine, kawai mubar musu Umma idan ta tashi saita had'a kokuma d'aya daga cikin su."

Ta na gama fad'in haka ta shige bathroom ba tare da ta jira abunda Fadwa zata ce ba. A bakin gado ta zauna Tayi jugum ' babu abinda take tunowa sai irin marin da Tasha wajen Yaya Khaleel.

"Anya kuwa Ilham zan iya bin shawarar ki kuwa?

Haka ta fad'a idanuwan ta cike da tsoro. "

Some *Minutes* *Later*

Bayan Ilham ta fito daga bathroom ne Fadwa ta shige cikin sauri ' Tukunna Ilham ta fara Shiryawa.

Yaya Farook saukowa yayi daga gado ' gami dayin mik'a sannan Ya fad'a bathroom cikin Sauri yayi wanka tare da yin Alwala, sannan ya fito yayi sallah. Bayan ya idar ne yaji cikin shi tamkar anyi mashi yasa aciki, Hakan yasa yayi saurin mik'ewa tsaye.

"Ashhh wace irin yunwa ce da sanyin safiya haka? "

Fita d'akin yayi cikin sauri, ya nufi kichen ' lipton ya fara nema baigani ba, ganin haka yasa Ya nufi d'akin su Ilham cikin sauri,

"Ke zo ki had'amun Tea insha yanzun nan Yunwa nakeji, "

Jitayi maganar ta daki zuciyar ta ' kallon shi ta juyo tayi, cikin k'unk'uni tace.

"To, "

Yaya Farook juyawa yayi ya koma d'aki ya cigaba da shiryawa, Ilham bayan ta kammala shirin tane ' ta je ta tsaya bakin Kofar bathroom,

"Fadwa dalla kiyi sauri, inba haka ba wallahi Tafiyata zanyi ' kinga har Yaya Farook ya sani aiki ko? "

Cewar Ilham,

"Ke naji ' yanzun zan fito dalla, "

Tsaki taja sannan ta wuce kitchen ' cikin d'an k'ank'anin lokaci ta had'a mashi ta kai mashi d'aki,

"Yaya Farook ga tea d'in nan, "

Nuni yayi mata da yatsa ' alaman ta aje saman side drower, Bayan ta ajene Ta juya ta wuce ' tana komawa d'aki ta iske Fadwa a zaune ta na Shafa mai,

"Wai ke Fadwa kanki d'aya kuwa? amma kinsan dai sauri mukeyi ko?"

Cikin hanzari ta tashi tasa kayanta sannan Tasha powder sama sama ' tukunna ta d'auki gelen ta yafa a kirji,

"Tow Am done. "

Ta fad'a rik'eda k'ugu ' sannan Ilham ta d'auki gelen ta itama ta yafa, suka fito parlor cikin sand'o har suka fita cikin garage ' Fadwa ce ta kwankwasa wa driver kofa,

"Ka fito mun shirya!

Cewar Fadwa, "

Ba tare da wani b'ata lokaci ba driver ya fito, ya bud'e motar sannan suka shiga ' tukunna yayi hone mai gadi ya bud'e gate d'in suka fice.

Bayan wuce warsu ne ' Yaya Farook ya fito rik'e da key d'in shi a hannu ya wuce Office,. Yana fita Umma ta fito daga sashen ta ita da Abba ' kallon dinning table tayi taga babu komai,

"ha'a inasu Fadwa ne? Ya haryanzu basu Had'a breakfast ba?"

Abba zama yayi a kujerar harabar parlor,

"Kila basu gama bane da wuri, "

Cewar Abba,

Umma d'akinsu ta nufa ganin basa cikine yasa ta wuce kitchen domin duba, nan ma haka ' cikin hanzari ta Koma parlor,

"Wallahi basa gidan, kardai sun tafi School ne yaran nan."

"Kinga bara kawai in wuce wajen aiki ' zan karya acen, tunda kikaga haka to sunda uzri ne a gabansu."

Yana gama fad'in haka ya tashi ya fita, Haka yai daidai da shigowar Yaya Khaleel parlor , a tsaye ya iske Umma tayi folding hannayen ta ' sannan ya zukunna cike da ladabi,

"Umma ina kwana! "

"Lafiya k'alau Khaleel ya gajiyan jiya? "

"Lafiya lau Umma ' Umma lafiya na ganki haka?

Yayi tambayar tare da mik'ewa tsaye,

"Hm Khaleel al'amarin yaran nan ne yabani mamaki, School suka wuce ba tareda sun had'a breakfast ba."

Cikin yanayi na mamaki yace, "what!! Lallai ransu zai b'aci yau, nasan wannan iskanci Wannan yarinyar ce Fadwa jikinta zai gaya mata. "

Umma zatayi magana yai saurin taren numfashin ta da cewa, "Umma karki damu nima gwani ne a kitchen ' da lafiyata da komai bazaki shiga kitchen ba ina kallo. "

Murmushi yayi mata sannan ya juya ya nufi kitchen ' indomie ya dafa cikin d'an k'ank'anin lokaci sannan ya kawo Ya aje a dinning table.

Umma na zaune a harabar parlor ' tana kallon kai da komo wanshi, saida ya gama jera komai sannan ya dawo ya zukunna inda take zaune.

"Umma ga abun karya war nan na kammala, "

To Umma ta ce sannan ta tashi ta nufi dinning table ta zauna ' cikin hanzari yayi sarving d'inta sannan shima ya zuba,

"Amm Umma Yaya ya tashi kuwa?"

"Gaskiya banji motsin shiba Khaleel,"

Tashi yayi ya nufi d'akin Yaya Farook, ya murd'a kofar yaji a kulle sannan ya juya ya koma parlor.

"Farook d'in na nan kuwa?"

Cewar Umma,

"a'a Umma k'ofar shi a kulle. "

"Ohh Hakane yaune zai fara shiga Office,"

OK kawai yace sannan ya maida kallon shi a kan plate d'in indomie d'inshi ya cigaba da ci.

*** *** *** *** ***

Around *11:30am*

Su Fadwa sun fito daga exam hall ' rik'e da handbag d'insu a hannu.

"Yanzu inda munsan zamu gama da wuri ' aida mun sanarwa Driver, "

Cewar Fadwa,

"ai bari kawai in kirashi ' don naga inada Number d'inshi. "

Ilham ciro wayarta tayi daga handbag d'inta tayi dailling number d'in Driver,

"Hello, kazo ka d'auke mu daga school ' don munyi closing. "

To kawai driver ya ce ' sannan ta kashe wayar, cikin hanzari driver yaje ya d'auko su daga school ' ya kawosu gida haka yayi daidai da fitowar Yaya Khaleel cikin Garage domin shan iska. Bayan su Ilham sun fito daga motor ne suna k'ok'arin shigewa gida, Yaya Khaleel ya dakatar dasu da cewa.

"Where did you think you're going to????"

Yayi maganar cikin yanayi na fad'a , a tsorace suka tsaya tare da juyowa suka kalleshi.

"Yaya Khaleel ciki zamu shiga,"

Cewar Fadwa.

"ciki ko? To kushiga!! Aike dama daga ganin kwayar idonki to baza kiyi kunya ba!!!. "

Fadwa kallon Ilham tayi suka had'a ido sannan ta sunkuyar da kanta k'asa,

"Ubanwa kuka mayar y'an iska??? Umma? Kokuwa Abba?? Ko kuma nida Yaya Farook?"

"Yaya Khaleel don Allah kayi hakuri ' zanyi maka bayani,"

Cewar Fadwa.

"Zakimin shuru ko sai nazo na tattaka ki? To bari kuji infad'a maku, da zarar kun shiga ciki kun aje wannan kima kiman handbags d'in naku ku zarce d'akina ku jirani. "

Tsoro duk ya gama cika Ilham idanuwan ta kuwa ' gabb suke da zubar da hawaye, d'ago kai tayi ta kalleshi gami dayin fuskar tausayi.

"Yaya Khaleeel please....

Bata kaiga k'arasawa ba ya daka musu tsawa,

"zaku b'ace mun da gani kokuwa?"

Da gudu suka shige cikin gida ' cike da tsoro.

Dedicated *To* *My* *Fan's*

□□□😜

[4/18, 3:55 PM] Maman Ussey😘: .....□□□□□□□

□□ *BABBAN...GIDA*□□

□□□□□□□

*_PERFECT_* *_WRITERS_* *_FORUM_*

© ```Written```

By

*_Seemaluvv_*□

21-22 pages□

Umma kai tsaye ta baro kitchen Ta nufi parlor Ilham da Yaya Farook suna biye da ita ' Suna Isa cikin Parlon suka iske Yaya Khaleel a zaune ya d'aura k'afa d'aya kan d'aya yana kallon TV, Jin Sallamar su ne yasa yayi saurin Juyowa ya kallesu tare da mik'ewa tsaye cike da Farin ciki, Cikin sauri ya rungume Yaya Farook Cike da jin dad'i,

"Yaya! Nayi kewar ku sosai wallahi"

Cewar Yaya Khaleel,

Murmushi yayi sannan suka sami waje suka zauna ' Yaya Farook yace,

"Khaleel kenan ai muma haka ' and Yanzu ai Kewa ya k'are tunda gaka a gida,"

"Hakane Yaya!"

Umma ce ta katse masu ' magana da cewa,

"O'!! Hanta da jini kenan, To ai saiku tashi Aje aci abinci ' don nasan Khaleel da yunwa ka shigo."

Dukkan su Dariya sukayi sannan suka mik'e tsaye da niyyar Zuwa dinning table Yaya Khaleel yaja kunnen Ilham gami da cewa,

"Ke haryanzu rashin kunyar ki tana nan ko? Bakisan kimun sannu da dawo wa ba ko?"

Saida ya bari Umma tafarayin gaba tukunnan ya zungure ta ' har saida ta fad'a saman kujera tukunna ya k'ara gaba. Cikin hanxari ta tashi kamar zatayi kuka sannan ta nufi dinning d'in.

Bayan zauna wansu ne Ilham tayi Sarving d'insu , ta zubawa kowa sannan ta zuba nata ' saida suka fara ci sannan Umma ta lura Fadwa bata wajen,

"Ilham me Fadwa takeyi ne ' da bazata zo taci abinci ba? "

"Bara inkira ta Umma."

Abin da Ilham ta ce kenan ta tashi ta bar wajen domin kiran Fadwa ' Yaya Khaleel kuwa Mamaki ne ya cika shi,

"Fadwa kuma? To bakuwa mukayi a gidan?"

Abinda ya ce kenan A zuciyar sannan ya cigaba da cin abincin.

"Kaii!!.. Umma abincin nan yayi dad'i wallahi Kodon na dad'e banci abincin ki bane? "

Cewar Yaya Khaleel,

Murmushi Umma tayi ' Cike da fara'a ta ce,

"Uhmm.. Khaleel kenan aibani nayi wannan abincin ba dakake ta zuba santi. "

"To Umma wane yayi? Kardai kice Ilham ce tayi abincin nan."

Tambayar ne ta bawa Yaya Farook dariya,

"To mai ka maida Ilham ' ina gidan nan ace bata iya abinci ba? Aiko da taci najaki."

Cewar Yaya Farook,

"Ai Ilham da Fadwa sune sukayi maka wannan girkin."

Tana gama rufe baki Fadwa da Ilham suka k'araso parlon ' cikin sauri bayan sun zauna ne Yaya Khaleel ya d'ago kai ya kalleta,

"Umma wannan ce Fadwa d'in? Ita kuma wacece? Na d'auka y'ar aiki ce ai."

Yayi maganar ya na kallon Umma, Nan Umma ta bashi labarin duk abinda ya faru ' da yadda akai ta dawo gidan da zama. Nan take tausayin ta ya kamashi ' cike dayin dana sanin Marin ta da yayi mata, Fuskewa yayi😎 sannan yace.

"welcome to our house Fadwa,"

"Yaya Khaleel aini ba bak'uwa bace kai zan cewa haka ai,"

b'ata rai yayi ya maida kallon shi ga abinci, Shi kuwa Yaya Farook Ita kawai ya ke kallo cike da shauk'i, Umma ta na gamawa ta tashi ta wuce sashen ta ' ganin haka yasa Yaya Farook mik'ewa da niyar Wuce wa d'aki tare da cewa,

"Dare yayi 8:00 yanzu ' idan kin gama kizo ki gyaramun gado na, don inaso inyi bacci ne. "

D'ago kai tayi ta kalle shi suka had'a ido tasan cewa da ita yakeyi, Sannan ya juya ya wuce. Ilham cikin hanzari ta kammala cin abincin ta tashi da niyyar tafiya ' Fadwa tayi sauri ta rik'eta,

"Please Ilham ki tsaya kid'an jirani na kusa gamawa.

Yaya Khaleel d'ago kai yayi ya kalli Fadwa, "

"A'a tunda kina zaune da aljani ai dole kice ta tsaya ta jira. "

Maida kallon shi yayi akan Ilham wacce duk ta gama tsorata ' cikin tsawa Yace,

"Come on ke kuma ki wuce kije ki kwanta ' tun kafin inb'ata maki rai a wajen nan. "

Da gudu ta k'arasa d'akin, Fadwa kuwa kasa cin Abincin tayi ta tsaya tana kallon plate d'in.

"Look! Idan kin k'oshi ne to ki tashi ki kwashe plates d'in don nagaji da ganin ki. "

Cikin sauri ta tashi ta hau hahhad'a plates d'in wajen, tana cikin haka ne ta ture Cup da ruwa aciki ' sam batasan ma tayi ba, haka ruwan nan yadinga malalewa har ya sauka a jikin Yaya Khaleel ' shigar ruwa yaji a jikin sa yasa yayi sauri mik'ewa tsaye,

"Kutma!! "

Jin haka yasa ta juyo ta kalle shi a razane,

"Fadwa jik'ani kikayi? Lallai jikin ki zai gaya maki."

"Yaya Khaleel don Allah kayi hakuri ' bada sani na nayi haka ba."

Matsowa yayi kusa da ita ya d'aga hannu zai sharara mata mari kenan Abba ya dakatar dashi da cewa,

"Karka kuskura , Koda wasa kada kasake ka mareta ' Au ashe muguntar taka tana nan ko? "

Abba ya fad'i haka yana k'arasowa wajen, Yaya Khaleel sauke hannun shi yayi Sannan ya watsa mata harara ' tare da cewa ,

"zamu had'u ai. "

Bayan Abba ya sami waje ya zauna ne ' yace,

"Me kika masa? "

"Abba Ruwane ya zuba a jikin shi by mistake ' shine yace... "

Bata k'arasa ba ta sunkuyar da kai,

"Kyaleshi ' karki damu dashi, Yanzu dai zo ki zubamun abinci na ' don yau na wuni ina aiki. "

To kawai ta ce sannan ta zuba abincin a plate ta aje mashi ' Tukunna tayi mashi sallama don bacci takeji, har ta kama Hanya zata wuce Yaya Khaleel ya ce.

"Ki biyoni da trolley d'ina d'akina"

Babu musu taja trolley d'in nashi tabishi dashi ' tafiya yake ta na binshi abaya, ganin sun wuce d'akin Yaya Farook ne yasata mamaki.

"Mun bani, i thought d'akin Yaya Farook zai kwana ' innalillahi kenan yanada d'aki dabam wanda bamu gyara shi ba. "

Haka ta fad'a a zuciyarta jikin duk yayi sanyi, suna isa bakin k'ofar Yaya Khaleel yasa hannu ya bud'e d'akin ya shiga kai tsaye sannan itama tashiga, tsayawa yayi yana k'arewa d'akin kallo ranshi abace ' ganin haka tasan cewa lallai yau zasuci ubansu hakan yasa ta fara zubda hawaye tunkafin ya yanke hukunci.

"Yanzu haka ake gyaran d'aki agarinku??"

shuru tayi ba tare da ta ce komai ba ' jin haka yasa shi juyowa a fusace,

"Fadwa ba dake nak....."

Kasa k'arasa maganar yayi ganin yadda hawaye kebin fuskarta, cikin hanzari ya matsa kusa da ita tare da cewa.

"Fadwa are you Okey?"

"Yaya Khaleel don Allah kada kabigemu ' wallahi aikine yayi yawa shiyasa muka manta da gyara d'akin, kuma ni nad'auka tare da Yaya Farook zaka rik'a kwana....."

Tana gama rufe baki yayi saurin rungume ta ' tare da shafa bayanta,

"is Okay! Fadwa ki daina wannan kukan ' tunda banyi bugunba tukunna. "

Yadda take ta mutsu mutsune ' ya gane cewa batason Hugging d'inne, Raba jikin shi yayi da nata gami da cewa,

"Yanzu dai kije ki d'auko min bed sheet, sai kizo ki samun a gadon inkwanta kafin gobe sai ku gyara."

Ok ta ce sannan ta juya ta fice cikin hanzari ' bata wani b'ata lokaci ba ta dawo d'auke da bed sheet a hannun ta ' ta mik'a mashi ya karb'a gami dayin kissing d'inta a goshi hakan yasa ta zaro ido,

"is a normal thing ' so don't fall in love with me, don nasan halinku Y'an nigeria ' saboda haka zaki iya tafiya."

Yana fad'in haka ta kama hanya ta wuce d'aki ta kwanta, Kwanciyar ta keda wuya ta tuna maganar Yaya Farook ' da sauri ta tashi zaune, Ilham dake kwance ta na chatting ne tace.

"Lafiya kuwa ?"

"Lafiya kalau kitchen zanje don k'ishi nakeji."

Ok kawai Ilham ta ce sannan Fadwa Ta tashi ta nufi d'akin Yaya Farook, Handle d'in ta murd'a taji a k'ofar a bud'e yasa ta shige cikin sauri. Akwance ta hangi Yaya Farook hakan yasa ta kiran sunan shi,

"Yaya Farook"

Jin yayi shuru ne yasa ta k'arasa cikin d'akin tare da cewa,

"To ko yayi bacci ne?"

Hayewa tayi har tsakiyar gadon shi ' sannan ta sunkuya tana kallon fuskar shi, bata ankara ba taji ya jawo ta jikin shi, lips dinta daff da nashi ' haka yasa ya matse ta sosai yadda bazata iya Kuccewa ba ' nan fa ido Ya raina fata,

"Yaya Farook na d'auka ko kayi bacci ne shiyasa."

Ta fad'a tana k'ok'arin janye jikinta,

"Yau anan nakeso ki kwanta ' Inaso ki d'ebemun kewa Fadwa,"

"Yaya Farook please ka bari intafi ' kasan banason irin wad'an nan abubuwan."

Ta fad'a tare da yi mashi magiya,

"Ke ! Am serious fa ' Karma ki bari raina yab'aci."

Ya fad'i haka cike da d'aure fuskar.

Murmushi tayi mashi tare da kashe mashi ido d'aya (wink), Sannan ta sa hannu a k'irjin shi ta fara yinmashi waiwayi a Wajen, Nan take ya farajin launin jikin shi yafara sauyawa ' cikin wata murya yace,

"Fadwa stop it ' kidaina yimin wannan abun please,"

"A'a"

Ta fad'a saida ra bari ya sakan kance sannan tayi wufff ta sauko daga gadon ' cikin Sauri har tana had'awa da gudu tabar d'akin, Yaya Farook Sai ninshi yakeyi yana mutsu mutsu.

D'akin su tashige a guje ' har saida Ilham ta razana,

"ke kuwa ina kika shiga? Don na je kitchen ban ganki ba,"

Fadwa kwanciya tayi gami da jan blanket ' sannan tace,

"Well, Ilham lambu naje."

"lambu da daddaren nan Fadwa?"

"yes ' fruit naje nasha, A tsorace na dawo shiyasa Ma kika ganni a haka."

"ke kika sani dai."

Abunda tace kenan ta maida kanta akan waya ' nan bacci yayi awon gaba dasu.

Dedicated *To* *My* *Fan's*

□□□😉

[4/18, 3:55 PM] Maman Ussey😘: .....□□□□□□□

□□ *BABBAN...GIDA*□□

□□□□□□□

*_PERFECT_* *_WRITERS_* *_FORUM_*

© ```Written```

By

*_Seemaluvv_*□

@ *_I_* *_proudly_* *_dedicated_* *_this_* *_page_* *_to_* *Jameesha* & *Husna*

*_Good_* *_Friends_* *_Are_* *_Hard_* *_to_* *_Find_* *_Difficult_* *_to_* *_Leave_* *_Impossible_* *_to_* *_Forget_* *_Nikam_* *_babu_* *_abinda_* *_zance_* *_sai_* *_godiya_*...*_dana_* *_sameku_* *_a_* *_matsayin_* *_Friends_*

25-26 *pages*□

Suna shiga cikin parlor suka iske Umma a zaune tana kallo ' basu san lokacin da suka tsugunna a k'asanta idanuwan su ciccike da hawaye,

" Umma don Allah kicewa Yaya Khaleel karya dake mu!

Cewar Ilham,"

Umma rage k'arar TV d'in tayi da remote sannan ta kalli Ilham,

"Ai bansan bakida Kunya ba sai yanzu Ilham ' inbanda kun raina mutane kwatafi ba tare da kun had'a mana abin karya waba? "

Sunkuyar da kai Ilham tayi Hawaye kawai ke zubo mata,

"Umma don Allah kiyi mana Hakuri ' wallahi Uzri mukeda shiyasa amma insha Allah haka bazai maimaita kanshi ba, "

Cewar Fadwa,

"Au kema zaki nunamin taki rashin kunyar kenan ko? Ai Fadwa koma wane irin Uzri ne daku ' ai kamata yayi Wani cikin ku yazo yaimun bayani, bawai ku kad'a kanku ku fita ba."

Umma na gama rufe baki Ilham taji saukar dundu a bayan ta, a kid'ime suka waiga domin suga waye ' Haba ido hudu sukayi da Yaya Khaleel, haka yasa suka tashi a guje tare da cillar da handbags d'insu zuwa d'akin shi.

Suna shiga d'akin shi suka zube a k'asa Cike da tsoro, Yaya Khaleel kwafa yayi gami da girgiza kai sannan ya biso.

"To banda mugun duka dai ' don nasan halinka. "

Cewar Umma,

Kai tsaye ya zarce d'akin shi ba tare da yacewa Umma komai, Cikin zafin nama ya bud'e k'ofar ganin su yayi a zukunne kowan nen su da hawaye sharkaf a fuskarshi, fuskar nan tashi a d'aure ya nufi wardrope dinshi ya zaro belt ' da Fadwa ya fara had'a ido sannan ya nufo kanta, ganin haka yasa tayi zambur ta mik'e tsaye.

"Yaya Khaleel don Allah kayi hakuri ' Karka dakemu please...."

Cikin kuka ta k'arashe maganar ta cike da shash shek'a,

"Ohhh Kokowa xamuyi koh? Aike dama nasan babu abinda bazaki iya ba.... "

Jikake zafff zafff ' saukar belt a bayan ta, Da gudu ta nufi wajen gadon shi ta rakub'e cikin kuka tace.

"wayyo!!! Yaya Khaleel don Allah kayi hakuri please forgive us....."

Komawa kan Ilham yayi wacce ko ina najikin ta rawa yakeyi,

"Ke dan ubanki ' da hankalin ki da komai, zaki biyewa wancen tsageran? saboda kin manta wanene Yaya Khaleel ko? To jikinki zai fad'a maki kuwa."

Sai da ya sauke mata belt shida a jikin sannan ' ya k'ara mata da hauri a jikin ta, saboda tsabar kuka Ilham ko hawaye ya daina fita daga idonta.

"Tashi ki fita ki bani waje ' idan ba haka ba saina kakkarya ki a wajen nan. "

Da gudu Ilham ta bar d'akin jin haka yasa Fadwa mik'ewa tsaye Cikin sauri zata fita, ya cafko ta A gigice ta juyo ta kalle shi.

"ina kike tunanin zaki? Ba tareda jikin ki ya gaya maki ba? Mara kunya!!!"

Jin saukar belt tayi a k'afa funta ' yasa tayin tsalle cikin rad'ad'i ta k'ank'ame shi jikinta sai rawa yakeyi,

"Ya..Yay. Yaya please kaimin afuwa ' wallahi zan iya mutuwa...."

Wani zirrr yaji tundaga k'afar shi har saman kanshi, shuru yayi nad'an lokaci sannan ya finciko ta da karfin tsiya har saida ta fad'a k'asa, a hankali yake takowa inda take ' ganin ya nufo ta da belt d'in ne hankalin ta ya k'ara tashi ,

"Yaya wallahi wannan ba plan d'ina bane Ilham ce tace muyi haka, please karka kasheni.

Jin haka yasa shi tsayawa cak ' tare da wullar da belt d'in a saman gado,

"Tashi ki fice mun da gani ' gobe idan Ilham tace ki shiga wuta sai ki shiga...."

Da sauri ta mik'e tsaye gami da had'awa da gudu ta fice daga d'akin, ba ta tsaya ko ina ba sai a saman gadon su.

Saida ta gama dawo wa normal sannan ta lura da Ilham rik'e da bucket d'in ruwan d'umi a hannunta tare da K'aramin towel tana gasa jikinta,

"Ilham?"

A gajiye Ilham ta juyo ta kalli Fadwa,

"Ya akayi?"

Fadwa tashi tayi ta zauna cikin jin zafin jikin ta,

"Meyasa Yaya Khaleel ya tsane ni?"

"Mtsww wannan wace irin banzar tambaya ce ' ni dalla ki kyaleni naji da d'aya mana aida kinsani kin tambaye shi kafin ki fito.!"

Ya tsine baki tayi sannan ta tashi ta fada bathroom don yin wanka da ruwan d'umi, ko da ta fito bata iske Ilham a d'akin ba nan ta d'aga kai ta kalli a goge,

"Ok! Lokacin girka lunch yayi 2:00pm Ilham na kitchen yanzu.

Bayan ta zauna agaban mirror ne ta fara gyara jikinta ' wayar ta tayi k'ara, cikin hanzari ta d'auka ganin Yaya Farook ne yasata yin picking cikin sauri.

"Hello Yaya.."

"Baby na yakike? Hope kina lafiya?"

A wahale ta ce, "lafiya kalau Yaya"

"Meyasa meki naji kamar bakida lafiya Fadwa!"

Jitayi kamar ta fad'a mashi abinda ya faru sai kuma ta fasa,

"Well, Yaya Farook babu komai ' is just that nad'an sami bacci ne d'azun. .

Ok yace tare da yinmata sallama sannan ya kashe wayar ' a tsanake ta tashi ta sanya kaya ajikin ta doguwar riga atamfa, sannan ta fito ta nufi parlor ganin Yaya Khaleel tayi a zaune ' nan take cikin ta murd'a ta juya xata koma ya dakatar da ita da cewa,

"Kije ki gyaramun d'aki na yanzun nan kuma ke kad'ai.

To tace sannan ta juya ta nufi d'akin shi, bayan y'an lokuta k'alilan ne ta dawo parlon ta zauna tare da cewa,

"Yaya Khaleel na gama.

ok ya ce ba tare da ya d'ago kai ya kalleta ba.

Around *2:30pm*

Ilham ta gama jera abinci da duk wani abun buk'ata a saman dinning table , sannan ta haura sama ta yiwa Umma magana ' hakan yayi daidai da dawo war Abba daga wajen aiki, Fadwa da Ilham da sauri suka tunkari Abba tare da yi mashi sannu ' sannan Fadwa ta karb'a bag d'in hannun shi ta kai sashen shi, Yaya Khaleel ya tare Abba cikin ladabi ya zukunna a gaban sannan ya ce,

"Abba sannu da dawo,"

Yawwa Abba ya fad'a sannan ya nufa dinning ya zauna, tukunna Umma ta fito cike da fara'a a fuskarta ta zauna gami da yiwa Abba sannu da dawowa, Ilham ce ta tashi donyin sarving d'insu Fadwa tayi saurin karb'ar Spoon d'in tare da cewa,

"Ai Abba nane so kibari na zuba mashi,"

Nan Ilham ta koma ta zauna gamida balla mata harara ' Abin haushi ya bawa Yaya Khaleel yasa yaje ya zauna awajen ,

"Ke kiyi ki zuba min yunwa nikeji!"

Ya fad'a a gadaran ce ' Abba ya kalle shi,

"banson takurawa fa Khaleel ' hannu biyu gareta ba takwas ba.

Saida Fadwa ta zubawa kowa tukunna ta nemi waje ta zauna ta fara bawa ciki abinci , saida kowa ya kammala sannan Ilham ta tashi ta tattara plates d'in wajen ta wuce kitchen dasu.

Umma da Abba tashi sukayi suka tafi sashen su ' Yaya Khaleel kuma ya fita harabar gida don shan iska, fitar shi keda wuya Yaya Farook ya dawo ' shigowa yayi tare da yin sallama, Fadwa da ke a zaune ta amsa mashi cike da fara'a.

"Baby na ke kad'aice a parlon?"

Yayi tambayar a gajiye gamida zaunawa,

"Eh ni kad'aice Yaya, In zubo maka abincin ne?"

Juyowa yayi ya sakar mata wani kallo ' tare da yin murmushi,

"Yes, but ki zubomin ki kawomin d'akina."

To tace mashi sannan ta yunk'ura ta nufi kitchen kasan cewar Ilham ta tattara komai ta kai kitchen, koda ta je kitchen babu kowa har Ilham ta gama ta wuce d'aki.

Cikin hanzari ta zuba abincin d'an daidai a plate tare da d'aukar roban ruwan sanyi ta nufi d'akin Yaya Farook ta aje masa a saman side drower sannan ta juya zata fita ya turo k'ofar, a tsora ce taja dabaya ta tsaya Yaya Farook ya k'araso daff da ita gami dayin mata kiss tare da rungume ta.

"i missed you so fucking much Fadwa!!"

Nan take ta saki wani k'ara cikin sauri ya saketa gamu da tallabo fuskarta nan yaga idonta yayi jaaa Alaman daf take dayin kuka,

"Babyna lafiya? Ko dai bakida lafiya ne?"

Yayi tambayar yana kallon Cikin idonta,

"Yaya Farook ' ka famamin inda aka dakeni ne d'azun!"

Nan ya waro manyan idon shi ' cike da mamaki,

"What!!! Waye ya dakeki??"

Ranshi abace yayi tambayar ' sunkuyar da kai kawai tayi hawaye na d'iga a hankali.....

Dedicated *To* *My* *Fan's*

□□□✌

[4/18, 3:55 PM] Maman Ussey😘: .....□□□□□□□

□□ *BABBAN...GIDA*□□

□□□□□□□

*_PERFECT_* *_WRITERS_* *_FORUM_*

© ```Written```

By

*_Seemaluvv_*□

www.Seemaluv.wapka.me

27-28 *pages*□

Sake tambayar ta yayi cikin tsawa,

"Nace waye ya dake ki!!!?

Ranta abace ta d'ago kai ta kalleshi, "

"Waye zai dake ni idanba Yaya Khaleel ba!! "

Jin haka yasa jikin shi yin sanyi ' Cikin d'an k'ank'anin lokaci ya ce,

"hm Fadwa ai bakwajin magana ne ' ni nasan Bro ba zai dake ki haka nan ba, sai idan kinyi laifi."

Tsayawa tayi tana kallon cikin kwayar idon shi cike da mamaki,

"I know that Yaya Khaleel d'an uwanka ne and ni ban fad'i haka da wata manufa ba and beside kai ne ka nemi kasani. "

fuuuu ta juya zata fita yayi saurin rik'e mata hannu,

"I know that you're hurt Fadwa ' but ki kiyi hak'uri bazan iya cewa Khaleel komai ba. "

"Is OK, na fahimta. "

Fizge hannun ta tayi ta fice daga d'akin , har ta nufi d'akin su sai kuma ta juya ta nufi d'akin Yaya Khaleel ' kasan cewar tasan cewar baya d'akin yasa ta bud'e Kofar a hankali gami da yin sand'o, ta na shiga ta tura ta rufe. Ciki ta k'arasa cikin izza ' ta hango Album a saman gadon shi tare da diarry d'insa a gefe.

Cikin sauri ta hau saman gadon ' gami da d'aukan Album d'in ta d'ora a cinyarta, (*Ohh* *Ni* *Seemaluv* *kodai* *Fadwa* *ta* *mance* *d'akin* *da* *shiga* *ne*?)

Budewa takeyi a hankali ta na kallon hotunan shi da abokanan shi mata da maza, haka taita kallon hotuna daga wanda zai bata dariya sai wanda zai bata haushi ' a haka har ta bud'o wani hoto, ganin hotun yasa gabanta fad'uwa.

"Dama Yaya Khaleel haka kake? Daman abunda kake tsina nawa a American kenan? Wannan kuma wacece to!!. "

Hoton cikakkiyar mace ce kyakkyawa ' haihuwar Uwarta, wacce babu kaya ajikinta ta na zauna. Cike da tsoro Fadwa ta rufe Album d'in tare da jan dogon tsaki,

"Mtsww wannan wace irin rayuwa ce? Yanzu shi kuma Yaya Khaleel me yakeyi da wannan picture d'in?"

Ta fad'a cike da takaici ' sannan ta jefar da Album d'in a gefe ta d'auki Dairy d'in. Bayan ta bud'e ne taga An rubuta, (Dear Diary...) A America ; ranar Litini ce na tafka babban kuskuren da ban tab'a tunanin zan tabka shiba a rayuwa ba, haka yasa duk idan na tuna dashi nakan zubda Hawaye.....

Fadwa bata kaiga k'arasawa ba taji an bud'o k'ofa bamm , da k'arfin tsiya hakan yasa ta razana ta mik'e tsaye cikin rawar jiki rik'e da Dairy d'in a hannun ta, Yaya Khaleel tsayawa yayi cak yana kallon ta cikin mamaki cen ya hangi Dairy d'in shi rik'e a hannun ta hakan yasa shi k'arasowa wajen ta cikin zafin nama da b'acin rai,

"Uban me kike min a d'aki? Ke wane irin stubbornness ke damun ki?"

Ya fad'a tare da kama kunnen ta,

"Ahhhggh Yaya Khaleel please am sorry ' zaka ciremun kunne!!!"

Ta fad'a Idonta cike da hawaye, Yaya Khaleel ya fizge diary d'in nashi gami da cewa,

"Bincike kike yimin dama? Da kikayi binciken ubanme kika binciko fad'amin, Iyee fad'amin nace!!!!"

Ya k'arashe maganar cikin tsawa, hakan yasa ta fashewa da kuka ' don kuwa tasan idan har tayi wasa to kuwa wani dukan zata sake sha,

"Yaya Khaleel don Allah ka tsaya kaji ' wallahi Allah ba bincike nake yi maka ba Yaya Farook ne ya ce inje in nemo masa biro, shine nazo nan ina dubawa....."

Ta na gama rufe baki ya d'auke ta da mari tasss, a gigice ta dafe wajen tare da sakin k'ara,

"Ahahhgg..."

"Ke!! Ni zakiyiwa k'arya da rainin hankali? Kaff d'akin ku babu mai Biro sai kin shigo nan? Iyeee ba tambayar ki nakeyi ba??"

Kwata kwata kasa magana tayi saboda kukan da yaci k'arfin ta, girgiza kai kawai takeyi Alaman a'a.

"In banda ke kin gama raina mutane ' Diary na a hannun ki sannan ki dubi tsabar idona kice Biro kikazo nema, Kakkarya kine kawai yau bazanyi ba Fadwa."

Sakin ta yayi ya nufa Wardrope d'inshi ganin haka ya bata damar fallawa a guje ta bar d'akin , kai tsaye ta wuce d'akin su cikin tsoro ta tura k'ofar ta rufe da key. Ilham wacce keta waya tun d'azu ne ganin halinda Fadwa ke ciki yasa ta yanke wayar ta cillar da ita saman gado, tayo kanta cikin hanzari.

"Lafiya Fadwa? Meyasa meki?"

Tayi tambayar tare da d'ago fuskarta, nan ta ga shedar hannu Alamun mari.

"Subhanallah meya sameki? Waya mareki! Halan Yaya Khaleel?"

Nin shi kawai Fadwa keyi sama sama ' saboda azabar da takeji a fuskar, Ilham rik'e hannun Fadwa tayi sannan tajata zuwa gado.

"Fadwa idan akwai wanda ya dace ki fadawa damuwar ki to ni'ce, "

d'ago kanta tayi ta kalleta da rinan nun idanun ta,

"Ilham d'akin Yaya Khaleel na shiga ni karan kaina bansan meya kaini ba, Bayan na shigane ya iske ni aciki shine yayi mun wannan mugun marin ' Ilham wai meyasa Yaya Khaleel ya tsane nine? Meyasa kokad'an baya d'aukata amatsayin k'anwar sa?"

D'an k'aramin tsaki Ilham taja sannan ta rungume Fadwa tare da bubbuga mata bayanta ,

